# AREWA24 TA KADDAMAR DA SABON SASHEN WASANNI DA AKE KIRA “A24 SPORTS”

**February 7, 2017** – Daga ranar 7 ga watan Fabrairu, 2017 kamfanin yada labarai na tashar gidan talabijin na AREWA24, mai yada shirye-shiryenta a harshen Hausa a kan taurarон Dan-Adam awa 24 na sanar da kaddamar da sabon sashen shirye-shirye, “A24 Sports.” Tun da aka kaddamar da tashar a shekarar 2014, AREWA24 ta kafa kanta a matsayin ta farko wajen samar da shirye-shiryen gida na ainihi a Arewacin Najeriya. Kirkirar A24 Sports, cigaba ne na aniyarta ta samar da mafiya kyawawa nshirye-shiryen gida ga masu kallonta. Wannan sabon sashin na A24 Sports zai kara samar da karuwar shirye-shiryen wasanni na gida da kuma taba ka lashe, tare da wasu ingantattun wasannin kasashen waje da muka samo izinin mayar da su cikin harshen Hausa.

Shugaban AREWA24, Jacob Arback, yana cewa ’Yan Najeriya suna kaunar wasanni. “A24 Sports zai fadada samar da sababbin shirye-shiryen da za su tallafawa shirye-shiryenta na wasanni guda biyu da take da su a yanzu, Taka Leda da Football Review. Wannan sabon shirin zai ba da himma ne a kan kungiyoyin wasannin da su ke a Arewacin Najeriya, ‘Yan wasan motsa jiki da masu horar da wasanni da kuma tattaunawar bayan fage da masu kallonmu a kan ‘yan wasa da kungiyoyin da suka fi so. Duk da cewa za a fi bawa kwallon kafa da kwallon kwando muhimmanci, A24 Sports zai tabo sauran bangarorin wasanni da taurarinsu sannan kuma da maudu’an da suka shafi yanayin rayuwar ‘yan wasan motsa jiki da guje-guje, abinci mai gina jiki da cusawa matasanmu maza da mata ra’ayin a dama da su a fannin wasanni.

Bugu da kari bayan samar da sababbin shirye-shirye a nan Arewacin Najeriya, A24 Sports zai kara da wasu sababbin jerin shirye-shiryen wasannin a kasashen waje: Domin kyautatawa jerin shirye-shirye ne da zai binciko mana yadda manyan ‘yan wasan duniya, irin su Didier Drogba, Aaron Mokoena da Samuel Eto’o, suka bata lokacinsu, suka bada gudunmowarsu ga mabukata, suka nuna halin jagoranci, karfafa gwiwa da niyya ta gari. Clubland ya zurfafa bayanai a kan tarihi, fitattun ‘yan wasa, masu horar da wasa da manyan karawar wasannin kungiyoyin premier league. Sannan, Legends yana ba da tarihi ne a kan faman da manyan fitattun masu motsa jiki na duniya suka sha, wadanda suka hada da Muhammad Ali, Tiger Woods, da sauransu.

Shugaban sashin tallace-tallace, Celestine Umeibe yana cewa "ma'aikatan daukar shirye-shirye da na tallace-tallacen AREWA24 na kara habaka tun daga farkon kafa tashar zuwa yanzu." "Wannan habaka ta sa muka dauki alwashi ga masu kallonmu na cigaba da kawo musu shirye-shirye masu nishadantarwa da suka fi kauna. Kaunar kwallon kafa da sauran wasanni a Arewacin Najeriya da Najeriya baki daya ya hada kawunanmu daga fannonin rayuwa daban-daban, a duk fadin kasar nan, daga dukkan yaruka da addinai."

Shirin A24 Sports ya fahimci bukatar al'ama na tallafawa da kuma bunkasa kungiyoyin wasanni, masu motsa jiki, masu horarwa, da kuma masu aiki tukuru a bayan fage don tabbatar da tallafawa matasa da kuma cusawa manya ra'ayin shiga a dama da su a fagen wasanni a Najeriya, musamman Arewacin Najeriya domin zama cikin koshin lafiya.

An kaddamar da AREWA24 a 2014 domin cike gibin shirye-shiyen da za su zama abin alfahari, akan kade-kade da wake-wake, al'adu, fasaha, girke-girke da wasanni a harshen Hausa, wadanda za su zama masu nishadantarwa da kuma nuni, da al'adu Arewacin Najeriya. A yau, AREWA24 ta zama hantsi leka gidan kowa, sama da mutane miliyan 80 masu amfani da harshen Hausa a Najeriya da Afirka ta Yamma suna samunta ta hanyar tauraron Dan-Adam na Eutelsat kyauta, da kuma tsarin Multichoice, DSTV (channel 261) da GOtv (channel 101). Bugu da kari, dukkannin shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta suna nan kyauta a YouTube da kuma mobile app dinmu. Shafukan sada zumunta na AREWA24, sun ba da cikakkiyar damar watsa manufofin shirye-shiryenmu da tattaunawa da jama'a a kan abin da ya shafemu duk a harshen Hausa.

**Game Da Arewa24:** AREWA24 (arewa24.com) gidan talabijin din Arewacin Najeriya ne na farko a tauraron Dan-Adam mai yada shirye-shiryensa 24/7 kyauta, wanda ke gabatar da shirye-shiryensa akan rayuwar Arewacin Najeriya, al‟adu, matasa, kasuwanci da nishadantar da iyali. AREWA24 ta dukufa wajen habakawa da kuma cike gibin da masu magana da harshen Hausa suka rasa na shirye-shiryen Hausa a duk fadin duniya, wadanda da yawansu sukan kama tashar AREWA24 ta hanyar yanar gizo domin ganin al‟adarsu da kuma ta sauran mutanen duniya. Ana dora shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta kowane sati a youtube.com/AREWA24channel, kuma tashar tana karuwa da masu kallonta ko da yaushe a AREWA24.com, Facebook.com/AREWA24, Instagram.com/AREWA24channel, da twitter.com/AREWA24channel.

AREWA24 tana kan EUTELSAT 16A, horizontal polarization, frequency 10804, symbol rate 30000 da kuma tauraron Dan-Adam na ACTV. Abokan huldar AREWA24 sun hada da Jordan Media City, Eutelsat da Globecast. Ana rarraba shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta a duk fadin Arewacin Najeriya tare da hadin gwiwar hukumar talabijin ta Najeriya (NTA). Tashoshin da suka fara gudanar da wannan hadakar ta NTA-AREWA24 sun hada da NTA-Abuja, NTABauchi, NTA-Kaduna, NTA-Kano, NTA-Maiduguri da NTA-Sokoto, kuma zamu ci gaba da kutsawa cikin sauran tashoshin NTA a Arewacin Najeriya gaba dayan wannan shekarar.